The Kumbotso Teacher Educator (KUTEJ):
A Journal of Multidisciplinary Studies
Vol 6.1 January 2015 ISSN: 1597-8796

# NAZARIN KALMOMIN ARO DA QIRQIRA A HARKAR WASAN QWALLON QAFA A DUNIYA

***Garba Abdu Gawuna DaSani Magaji***
Department of Hausa
Sa'adatu Rimi College of Education, P.M.B 3218
Kumbotso, Kano

**Tsakure**

*Wannnan takarda mai taken; "Nazarin Kalmomin Aro da Qirqira a harkar wasan Qwallon Qafa a duniya" ta tattauna ne a kan tarihin samuwar wasan da qa'idojinsa, sa'annan ta ci gaba da taqaitaccen bayani a kan qungiyoyin qwallon qafa na qasashen Turawa da gudunmawar da kafafan watsa labarai suke bayarwa, wajen yaxa labarin wasanni. Sa'annan takardar ta ci gaba da bayani a kan kalmar aro da yadda ake qirqira a cikin Harshen Hausa. Daga qarshe takardar ta kawo misalan kalmomin aro da na qirqira da ma'abota kallon wasan ke amfani da su domin nishaxantuwa.*

## Gabatarwa

A qasar Hausa a kan ce qwallon-qafa, Tamaula. A Arewacin qasar Hausa kuwa, a kan ce kwanvala. A

turance kuwa ana cewa ball, football, ko soccer. Larabawa kuwa suna cewa kurra, kurratul qadam.

Qwallon-qafa daxaxxen wasa ne, da yake da magoya baya da yawa, ana yin sa ne a dukkan qasashen duniya. A kwai a qalla mutane sama da miliyan ashirin a duniya da suke yin was an (Encyclopedia Americana vol. ii p. 531). Ana yin wasan qarshe na cin kofin duniya, da (olamfik) (olympics) duk bayan shekaru huxu, kuma ana nunawa a kafafen yaxa labarai kamar su talabijin, radiyo, internet, da dish. Inda biliyoyin mutane suke kallo da sauraro. Babbar sitadiyam (stadium) a duniya ita ce Marakana da ke qasar Brazil mai xaukar mutane sama da dubu dari biyu. Encyclopedia Americana, Vol II (p.531).

**Yadda ake Wasan**

Vangarori biyu suke buga wasan, kowanne vangaren mutum goma-sha-xaya. Xaya mai tsaron gida ne, mutane goma a tsakiyar fili, sanye da riguna mabambanta.

Akwai alqalin wasa wato Rafali (referee) kuma wasan yana da tsari da qaidoji. Wasu daga cikin qa'idojin su ne:

Free – kick → Bugun Tazara
Foul → Lokacin da aka tava qwallon da hannu ko a kabugi xanwasa sai a ce mutum ya karya dokar wasan saboda haka ya yi foul.
Penality →Bugun daga kai sai mai tsaran gida
Corner → Bugun gefen raga ko jifa
Throwing → Jefawa da hannu
Goal kick → Bugun gola
Red card → Katin rashin xa'a, mutum ya karya babbar dokar was an (jan kati)

Yellow card→Katin rabin rashin xa'a (yalon kati)

Yayin da shi kuma qwallon qafa na garuruwan turawa wato league-league. Ana yin sa ne duk shekara, kuma yana xaukar a qalla watanni goma ana bugawa. An fara wasan qwallon qafa na duniya a shekarar 1930, wanda qasar (Uruguay) ta karvi baquncinsa kuma ta xauka. Shi kuwa wasan (Champion league na Europe) an fara shi a (1955) inda club din Real Madrid ya xauka a karo na farko (Weekly Trust 2014).

A can baya kallon qwallon qafa sai an je sitadiyam (stadium), amma yanzu saboda juyowar zamani akwai gidajen kallon wasan a kan sa talabijin, a biya kuxi a shiga kuma a kalla. Wato (viewing center) masu wannan kallo su kan yi barkwanci a tsakaninsu a yi wasa da dariya. Wani lokacin a kan yi mummunan tashin hankali har ta kai ga rasa rai. A shekarar 2010 a Fagge (Kano) wani yaro ya kashe maqwabcinsa a kan musun ball, bayan Bercelona ta doke Madrid. Haka a (2012) lokacin da Chelsea ta doke Bayernmunich, wani yaro a Lagos ya kashe abokinsa ta hanyar caka masa kwalba. A babban Dodo Zariya (2013) an samu kisan kai kamar yadda Jaridar Aminiya ta wallafa.

A kan haxiyi zuciya a mutu kamar yadda jaridar Daily Trust (Sept. 23, 2014: 16) ta wallafa; "*foot baller dies after Frank Lampard equalizer*". Wato wani xan qwallo ya mutu lokacin da xan wasa Frank Lampard ya farkewa bangarensa.

Haka wani mutum xan kimanin shekara 42 mai suna Ray Dunning ya faxi matacce a lokacin da ya tabbatar kulob

xinsa ya samu komawa baya (relegation) a gasar rukunin 'yan dagaji (Champion's League), Aminiya 9 May (2014: 3a).

Haka, a Gayawa, qaramar hukumar Ungogo, Kano "wani ya kashe abokinsa saboda musun ball ta hanyar soka masa wuka a qirji". Rahama Radio (10-10-14) (8.830).

Haka kuma wani rahoton; "*man slumps, dies over Manchester United defeated*" Daily Trust (Dec 28, 2015: 42). Wato wani mutum ya yanke jiki ya faxi kuma ya mutu bayan kulob xin da yake goyon baya wato Manchester United ta sami rashin nasara.

Akwai qungiyoyin wasannin qwallon-kafa da dama a qasar turai. Amma waxanda a kafi kallo a qasar Hausa sune:

- Premiership, wato England league- akwai kulub kamar su: Chelsea, Manchester United, Arsenal, Liverpool, da sauransu.
- Serie A, wato Italian league Inter millan, A.C Milan da sauransu.
- Ligue I, wato French league akwai P.S.G, Monaco da sauransu.
- Bundesliga, German league, akwai Bayernmunich, Shalk 04 da sauransu.
- Portuguse, wato Portuguse League, Porto, Sporting Lisbon da sauransu.
- Laliga, wato Spain legue akwai kamar su Bercelona, Real Madrid Atlectico Madrid da sauransu. Weekly Trust April (2014:35).

Akwai kafafen yaxa larabai na gida da na waje da suke gudanar da shirye-shirye a kan labarin wasanni ga su kamar haka:

- Radio France International (RFI) - 7:30-8:00am Labarin Wasanni Radio Deutchwalle German, Laraba 7:15pm
- Labaran wasannin tsakiyar mako - Radio Kano 1:30 2:00pm ranar Laraba
- B.B.C labaran wasanni, Ranar Talata 8:57pm
- Voice of America litinin, labarin wasanni 9:40pm
- Radio Kano labarin wasannin Qarshen mako 9:00am 9:30am ranar Lahadi
- Freedom Radio tare da haxin gwiwa da B.B.C London inda suke kawo sharhin rahotannin waasanni Ingila kai tsaye wanda Mamman Skipper yake gabatarwa.
- Akwai dandadalin qwallon qafa wazobia FM 5-5:30pm da dai sauransu.

**Ma'anar Aro a Harshe**

Akwai masana da dama da suka, ba da ma'anar Harshe da kuma abubuwan da suka dangance shi dangane da asali da kuma bunqasar sa, da yadda al'ummomin na duniya suke tinqaho da alfahari da shi. Mutum a ko da yaushe yana yin zancen zuci don son ya fassara abin da ke zuciyarsa na farin ciki ko baqin ciki ta hanyar bayani da harshe.

A salin kalmar aro kalma ce ta larabci da hausawa suka aro ta daga harshen. Su kai hankaka mai da xan wani naka. Kalmar aro asalinta balarabiya ce wadda aka aro ta

daga kalmar *Ariyatun* ( عارية) to sai hausawa suka datse mata farko, a matsayin ma'arif wato daga (Al-*Ariyatu*) (العارية), amma a matsayinta na kira wato '*Riyatun'* sai a kai mata haruffan qarshe guda biyu wato ya da tu sai ya koma Ari, misali Ari- a matsayin shuxaxxen lokaci (General Past Tense GP).

Yaa ari mota (GP)

Ya ari mota (RP) amma ma'anar kalmar aro. Garba A. (2009)

Shi kuma Imam, G. (2009) ya bayyana ma'anar kalmar aro da xauko kalmar daga wani harshen a shigar cikin jerin kalmomin wani harshen daban.

A taqaice dai aro na nufin a xauki wata kalma daga wani harshe a shigar da ita cikin wani jerin kalmomin wani harshen na daban.

## Qirqira a Harshe

Qirqira ko ginin kalma fanni ne na yin nazari a kan yadda ake gina kalma. Abubakar, A. (2001) ya ce, "kalma qera ta ake yi a ilmince", wato kada mu xauka ginin kalma ana yin sa ne da wasu kaya na daban, a'a ana gina ta ne ta hanyar ilimi. Wannan ginin ana yin sa ne da wasu tubalu na musamman waxanda ake kira qwayoyin ma'ana. Duk wata kalma da aka sami tana xauke ne da qwayoyin ma'ana. Akwai turkakkiya, akwai kuma 'yantacciya. 'yantacciyar qwayar ma'ana ita ce wadda take iya zama ita kaxai ta bayar da ma'ana. Tana kuma iya haxuwa da wasu qwayoyin ma'anarsu tayar da

wata kalmar. Misalin qwayoyin ma’ana ‘yantattu su ne: zo, gida, sha, tafi, da sauransu.

Ita kuwa qwayar ma’ana turkakkiya ita ce qwayar ginin kalma wadda ba ta iya zaman kanta, sai an haxa ta da wata qwayar kalma sa’annan ta bayar da ma’ana. Misalin irin waxannan qwayoyin ma’ana sun haxa da; i, e, a, inya, ai, wa, aje da sauransu. Duk waxannan kalmomi, ka lura da qarqashinsu. Irin waxannan qwayoyin ma’ana su ne turkakku; shixi, shuxiyaa, shuxayee, xalibi, xalibaa, xalibai, kore, koriya, koraye, muguu, muguwar, gida, gidaje, da sauransu (Abubakar, 2001).

Misali dubi kalmar:

a. Yaro – qaramin mutum, namiji
   Yar – saiwar kalma
   - o - qwayar ma’ana mai xauke da ma’anar namiji.
b. Yar – saiwar kalma
   - Inya – qwayar ma’ana mai xauke da ma’anar mace.
c. Yar – saiwar kalma
   - a – qwayar ma’ana mai xauke da ma’ana fiye da xaya.

Akwai xafi iri uku a ginin kalmar hausa su ne; xafa goshi, xafa ciki da kuma xafa qeya.

1. **Xafa – goshi**: shi ne qarin da ake yi wa saiwar kalma daga gabanta. Misali, magini, maqeri, bature, da sauransu.

2. **Xafa – ciki**: shi ne qarin da ake yi a cikin saiwar kalma don a gina wata kalmar. Misali

| **Kalma** | **Saiwa** | **Jam'i** |
|---|---|---|
| Birni | birn | birane |
| Kulki | kulk | kulake |
| Turmi | turm | turame |

3. **Xafa-qeya**: shi kuma qari ne da ake yi a qarshen saiwar kalma don a gina wata kalmar. Akwai misali;

   Yaro yar - yara

   Noma nom nomau da dai sauransu

   (Sani, M. 2002)

Wata hanyar da ake amfani da ita domin qirar kalma ita ce tsirar kalma. Wannan nau'i ne na ginin kalma, a inda ake xafa wata qwayar ma'ana a jikin saiwar kalma. A sakamakon haka sai a fito da wata kalma sabuwa wadda rukunanta na Nahawu ya sha bamban da ta farko. Abubakar, A. (2001)

Qari bisa ga wata hanya da ake qera kalma a Hausa ko qirqira ita ce harxantawa. A irin wannan tsarin akan haxa kalmomi biyu ne ko uku ko fiye mabambanta don a tsayar da wata sabuwar kalma mai sabuwar ma'ana (Sani, M. (2002). Misali:

a. **Suna** a haxa shi da wani **sunan**.
   Azumi + jemage = azumin jemage
   Hava + kada = havar kada
b. **Suna** a haxa da **aikatau**.
   Keke + xinki = keken xinki
   Tari + shiqa = tarin shiqa
c. **Aikatau** a haxa da **suna**.
   Tuma + qasa = tuma-qasa
   Ruxa + kuyangi = ruxa kuyangi

d. **Aikatau** a haxa da **aikatau**.

Gutsuri + tsoma = gutsuri tsoma

Faxi + tashi = faxi tashi Abubakar, (2001)

A qari bisa ga wasu qarin hanyoyin da ake samun qirqirar kalma ita ce "Ninki". Shi ninki wata hanya ce ta samar da sababbin kalmomi. A wannan tsarin, akan nanata kalma ne, a dalilin yin hakan kuma sai a sami sabuwar kalma mai sabuwar ma'ana. Akwai ninki iri biyu; cikakke da ragagge (Sani, M. 2002).

Cikakken ninki shi ne wanda ake ninka kalma gaba xayanta, misali;

| **Kalma** | **Cikakken Ninki** |
|---|---|
| Sannu | sannu-sannu |
| Buhu | buhu-buhu |
| Uku | uku-uku |

Shi kuwa ragaggen a irin salon, wani yankin kalma ne ake ninkawa, misali:

| **Kalma** | **Ragaggen Ninki** |
|---|---|
| Taka | tattaka |
| Biyu | bibbiyu |
| Karya | kakkarya |

Waxannan kaxan ne daga cikin hanyoyin da ake qirqira da samar da sababbin kalmomi a cikin harshen Hausa. A iya samun wasu hanyoyin don samar da sababbin kalmomi da qirqira a cikin harshen bayan waxannan.

## Misalan kalomomi da yankin Jimla a Harkar Qwallo

An wayi gari masu kallon qwallon qafa a Kano sukan yi amfani da qirqirarrun kalmomi wajen gwarzanta qungiyar da su ke goyan baya wanda yake haifar da

nishaxi, barkwanci, kai har ma da zummunci duk da cewa, wani lokacin akan sami hargitsi, hayaniya kai har ma da kisan kai kamar yadda ya zo a bayanan da suka gabata.

| **Kalma** | **Abin da ake nufi** |
|---|---|
| Kaya- kaya | ya yin da aka ci wani ko wata qungiya akan faxawa magoya bayan su wannnan kalma, wato sun xauki dakon qwallo. |
| Rubin- kazan | sun sami wannan suna ne a 2006 lokacin wasan zakarun Turai, mai horar da su ya na rige da carbi a |
| Liverpool maja | suna da yan wasa ne da su ka zo daga nahiya daban – daban. |
| Wankin hula ya na neman kai su dare | akan faxi wannan zancen ne, lokacin da wata qungiya ta rena wata, tana ganin ta fi qarfin ta, amma har dab da tashi ba su iya zura masu qwallo a raga ba. |
| Ya kai hari | lokacin da qiris xan wasa ya jefa qwallon a ragar abokan karawasa. |
| Ya addabe su | akan faxi wannan kalma ne lokacin da xan wasa ya fara kai hari dab da ragar abokan kara warsu |
| Ai kata i' ne | ma’anar ya iya wasa, gwani ne, a wani lokaci a kan ce ai shege ne. |
| Shi ne bayan | lokacin da xan wasan baya ya faye tare harin abokan karawarsa, ma’ana wanda ya tsaya a baya ya hana a kaiwa golarsa hari. |

| | |
|---|---|
| Shi ne gaban | wanda ya faye kai hari zuwa ragar abokan karawarsu. |
| Tsakiyar su a buxe take | ma'ana 'yan wasan tsakiya wato (mid-fielders) ba su yin abin da ya kamata wajen hana abokan karawarsu ratsawa su wuce. Domin kai masu hari. |
| Baya ba zani | lokacin da 'yan wasan baya suka gusa gaba domin kai hari kafin su dawo su ma aka kai masu. |
| Ba su da gola | ma'ana mai yi musu tsaran gida, bai iya aikin sa ba. |
| Su na da gola | mai tsaran gida gwalkifa ya iya aikinsa, wato gwani ne |
| Kai kaxai gaiya | Ana amfani da wannan kalma, wajen shahararrun 'yan wasa, kamar Messi, Ronaldo, wanda indai an yi wasa sukan saka qwallo a raga. Wani karon ma har fiye da sau xaya. |
| Ta qare masu | akan faxi wannan kalma lokacin da karsashin wani shahararriya qungiya ya ja baya, kamar abin da ke faruwa da Manchester United. A yanzu ko Chelsea |
| Mai Arsenal | akan faxawa magoyin bayan wannan qungiya wannan suna. |
| Mai Manchester | a kan faxawa magoyin bayan wannan qungiyar wannan suna. |
| Real Madrid madarar qwallo | a kan faxawa wannan kungiyar sunan saboda qwarewar su wajen qwallon qafa, ma'ana ball zalla. |
| Madara ta zama gari | lokacin da gwaninta, da karsashi na qungiyar Madrid ya ja baya sai akan |

| | |
|---|---|
| | gayawa magoya bayan su wannan kalmar. |
| Arsenal samarin Winger | a kan faxa masu wannan suna saboda matasa ne. Winger xin sunan mai horar da su ne. |
| ‘yan kofi haram | Wannan suna a kan faxawa magoya bayan kulob xin Arsenal don ba su iya yin nasarar cin wata gasa. |
| ‘yan dagwai-dagwai | Ma’ana ‘yan Arsenal matasa ne yara duk kusan kansu xaya, a kan ce masu samarin Winger. |
| Chelsea yan qato da gora | saboda yan wasan su suna da girman jiki, kuma su kan doke qanana. |
| Blues | Ana nufin kulub xin Chelsea, saboda kayan wasan da suke sawa duka ruwan bula ne. |
| Club xin Lyon kanukawa, yan- tavare. | a kan faxa masu wannan suna, saboda qaramin kulub ne, da ba zai iya kawai wani, mataki ba, amma idan ana so a yi nasara a kan su don a kai wani mataki sai su dage su qi yarda. A sami nasara a kansu. Saboda haka mai son yin nasara a kansu don ya kai wani mataki sai ya rasa |
| Depotivo kowa goma, dalla-dalla | lamba goma a fagen qwallo shi ne mai raba qwallo, to su yan wannan kulub, kowa raba qwallo yake, har kuma ka kasa gane wane ne goman. |
| Bercelona, gidan ban kashi. Barca ba sani, ba | kasancewa su da duk wanda suka kara sai sun yi nasara akan sa. Ma’ana ba bu wata qungiya a gabansu da suke shakka. |

| | |
|---|---|
| sabo. | |
| Totenham fararen balbelu | Ana faxa masu wannan suna ne saboda suna sa fararen kayan wasa. |
| A.C Milan gidan tauri, ko gidan Gajiyyayu, ko a ce Jigawa tarin Allah | a kan faxa masu wannan su na ne saboda duk wani xan wasa da ya tsufa, ya kusa ritaya sai ya koma, can don ya yi wasan qarshe. Kuma duk da haka ba kowacce qungiya ba ce take Nasara a kan su ba kai tsaye. |
| Roma gidan tauri | qaramar qungiya ce amma ba kasafai manyan qungiyoyi sukan sami nasarar akan su kai tsaye ba. |
| Jeventus, zebra | rigar sawar su ta zama kamar jikin zebra, wato na raqumin dawa, baqi da ratsin fari |
| Ruwa-ruwa ko tuvus-tuvus | ma’ana akan faxawa qungiyar da akan sami sauqin nasara a kan ta wannan suna. |
| Mun dafa su | a kan faxawa qungiyar da akai nasara a kanta cewa an dafa ta. ma’ana an yi Nasara a kanta |
| A.C. Milan majalisar dattawa | a kan faxawa wannan kungiyar wannan sunan ne saboda tsofaffin ‘yan wasa da suke da su waxanda sun kusa ritaya. |
| Man-city yan rusau | a kan faxa masu wanan suna ne, saboda duk wanda suka haxu da shi su sukan bige shi |
| Dortmand ‘Yan karota | wannan kungiyar a qasar Jamus ta ke, akan faxa masu wannan suna saboda kayan wasan da suke sawa na baqin |

| | |
|---|---|
| | wando da yellon- riga. Ya so ya yi kama da kayan wata qungiya mai Lura da Hanya a Kano(Nijeriya). |
| Bercelona ‘yan Boko Haram | a nijeriya boko haram wata qungiya ce da take faxa da ‘yan sanda ta doke su. Su kuma Bercelona suna doke Madrid, su kori Madrid ana ce masu ‘yan sanda. |
| Madrid yan sanda | ana faxa masu wannan suna saboda duk wata qungiya da ta kara da su za su bugeta su kamata amma Bercelona su ne kaxai suke iya buge su, su sami nasara a kansu.. |
| Sunderland mayun draw | wannan qungiya a ingila take duk sanda su ka yi wasa sai dai a tashi babu nasara a ko a a wanne vangare. |
| Stock city mayun throwing | wannan qungiya a ingila take, ta gwanance wajen jifa da hannun. |
| Sun ci kubeji | akan faxi wannan kalma ne lokacin da wata qungiya ta jefa qwallo a ragas abokiyar karawar ta amma, kuma ta fi shan wahala, ai ta kai ma ta hare-hare, kamar ba su ne ke da nasara ba. |
| Canjaras | an tashi babu ci ga kowanne vangare |
| Kilin gol | an ci qwallo mai kyau babu inda-inda |
| Ya cika da imani | ma’ana xan wasan da ya kamata, ya bar qwallo saboda shekaru. Kuma yayi hakan tun jama’a suna qaunarsa. |
| Xan caca ne | Ma’ana mai sarrafa qwallo yadda ya kamata |
| Raba masu | a sami nasara a kan wata qungiya |

| | |
|---|---|
| aiki | |
| Kowa ya iya ya huta | a kan faxi wannan batu ne lokacin da akai wasa mai kyau, kuma a ka sami nasara. Musammman ga manyan qungiyoyi: kamar su Bercelona da Madrid |
| Kunnen doki | an ta shi babu ci, ba bu wata qungiya da tai nasara a kan yar uwarta |
| Ai sun yi cefane | ma'ana sun sayi zarata gwanayen 'yan wasa |
| Cefane ba shi ne miya ba a sami wadda ta iya girki | akan faxi wannan batun ne ga qungiyar da, suka sayi zarata, gwanayen 'yanwasa amma sun gaza samun nasara. Duk da waxannan |
| P.D.P | a kan faxi wannan batu ne lokacin da wata qungiya take ganin an yi mata son kai. P.D.P jam'iyyar siyasa ce a Nijeriya wadda lokacin da take mulki ta gwanance a wajen maguxin zave. |
| Rafalin Manchester | wannan wani rafali mai suna (wheb) xan kasar Ingila, shi ne ya busa wasan cin kofin duniya na qarshe shekara 2010. Ana faxa masa wannan suna ne saboda duk lokocin da ya busawa Manchester suna samun nasara. |
| Ramzi ya yi almubazaranci da qwallo | a kan faxi wannan kalma ne, lokacin da xan wasa ya je dab da raga, amma ya kasa jefa ta ciki, kuma hakan ya xauki hankalin jama'a. |
| Zawarawa yan Mancherster | akan faxawa Manchester wannan suna saboda yawanci yan wasan su sun xan manyanta, wannan ya sa ba su samun |

| | |
|---|---|
| United | nasara sosai. |
| A ci gaba da gashi suya sai ranar Sallah | a kan faxi wannan batu ne lokacin da aka kai hare hare, a ka yi ball ta burge ‘yan kallo, a kanyi kuwwa sai a faxi wannan batu. |
| Sai basa | mai goyan bayan kulub xin Bercelona na kasar spain shi ne yake faxin wannan |
| Sarki ya hana dawa tsayuwa | a kan faxi wannan batu lokacin da wani xanwasa ya sami wani a tsaye, ya make shi ya faxi. |
| Dakon tebur | a kan faxi wannan ne lokacin da wata qungiya ta ringa samun nasara har ta yi na xaya a jadawalin wasan, amma daga baya samun nasarar su ya dushe suka yi yo qasa |
| Ya yi moxa | a kan faxi wannan ne lokacin da xan wasa baya ya bugi qwallo, mai makon qwallon yayi gaba, sai ya dawo baya. |
| Qafa xaya gare shi | xan wasa mai amfani da qafa xaya wajen buga qwallo dama ko hagu, don akan- sami xan wasan da yake amfani da dukan qafafun sa biyu. |
| Qafa biyu gare shi | xan wasan da zai iya buga qwallo da duk qafafuwansa biyu |
| Ba su da ‘yan baya | suna da yan baya masu rauni |
| Suturaika ne | xan gaba mai cin qwallo |
| Defenda ne | mai tsare baya |
| Sai Madrid | sai club xin Madrid |
| Raga janba | kulub din da yake da sauki a sami |

| | |
|---|---|
| | nasara a kansa |
| Red devil | a na nufin Manchester united |
| Fara da baqa | a kan yiwa ball wannan kirarin don yau nasara gobe akasin haka |
| Ya yi bidia | ya yi abu mara kyau da qwallo |
| Leda | ball, qwallon qafa |

**Kammalawa**

Qwallon qafa daxaxxen wasa ne a duniya wanda yake da magoya baya da yawa. A can baya kallon qwallon qafa sai a sitadiyam, amma yanzu saboda zamani akwai gidajen kallo (viewing center). Masu wannan kallo su kan yi barkwanci a tsakaninsu a yi wasa da dariya, a wani lokkacin a kan yi mummunan tashin hankali, wannan ya sa aka sami bunqasar Adabi da Harshe. A cikin harshen Hausa, ma'ana sanadiyar wannan kallon wasa an sami sababbin kalmomin aro da kuma qirqirarrun kalmomi da suka daxa bunqasa harshen Hausa.

**Madogora**

Abdullahi, G. (2009). Asalin aro, ma'anarsa da ire-irensa. Sashen koyar da harshen Hausa, Kwalejin shari'a da nazarin addinin Musulunci (School of Legal Studies, Kano).

Abubakar, A. (2001) An introductory Hausa Morphology, Jami'ar Maiduguri.

Bayero University, Kano (2006) Kamusun Hausa. Zaria Ahmadu Bello University Press.

Daily Trust News Paper (2014). Published by Media Trust Limited Cooperate office: 20 P.O.W

Mafemi Crecsent off Solomon Lar way Utako District Abuja.

Dikko, I. da wasu (1991) Kamushi na adon maganar Hausa. Zaria Northern Nigeria Publishing Company.

Encyclopedia, Americana Arête Publishing Company Inc. Vol ii (1981) Princeton New Jersy.

Garba, C. Y. (1984). Nazarin Hausa don qananan makarantun sakandire. Northern Nigeria publishing company.

Hira da Anas Iliyasu (2014) Dalibi mai ra'ayin kallon kwallon kafa a Kano a gidansu ranar 12/9/14 da karfe 12:24pm

Jaridar Aminiya (2015) Media Trust Limited ofishi: 20 P.O.W Mafemi Crescent, da zarar an saki titin Solomon Lar, a yankin Utallo da ke Abuja.

Mathews Peter (1997) Morphology an introduction to the theory of word structure, served edition Cambridge University press.

Saeed, J.I. (1997) Semantics, USA Blackwell publishing.

Sani, M.A.Z. (2002). Alfiyyar Mu'azu Sani Kano; Benchmark publishers.

The new Encyclopedia Britinnica. William Benthery publisher Vol (9) (1981)

Weekly Trust (2014) Published by Media Trust Limited Cooperate office: 20 P.O.W Mafem Crescent off Soloman Lar way at Kano District Abuja.